

 

An yi wata kaza.

Kaza ta ga aku.




Jikin aku na da kyau.

Kaza na son jikin aku.



Kaza ta lura da aku.

Aku na sama a itace.



Kaza ta lura da aku.

Aku na cin fure.



Kaza ta hau itace.

Kaza tana cin fure.






Kaza na kan itace.

Kaza tana son jikin aku.



Kaza ta ci fure.

Zawo ya kama kaza.



Jikin kaza bai canza ba.

Kowa da jikinsa.